# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da



# Mai Arziki, Marar Arziki


**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: M. Maillot; Lazarus Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: M. Maillot; Sarah S.**



**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**



**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**




**Yesu ya sani cewa yawancin shugabanin addini suna son kudi fiye da yadda suke son Allah. Sai ya fadi wani abu da ya faru da mutane biyu, da kuma yadda banzan abu ne ka zama mai arziki kuma babu Allah. Arziki ba zai sayi rai na kasance tare da Allah a samaniya ba.**



Akwai wani mutum mai arziki wanda yana da riguna masu kyau masu tsada. Yana yin ado kamar sarki.



3

Wannan mai arzikin yana ci da kyau. Kowane abinci ya zama kamar ana wani babban biki ne. Yana da kudi da yawa wanda zai iya sayan kowane abin da yake so na abincin safe, da na rana, da na yamma – ko ma abin ci na tsakani.



4

A bakin kofar gidan mai arzikin nan akwai wani marar arziki kwanciye, babu lafiya, yunwa na so ya kashe shi. Sunansa Liyazarus.



5



Liyazarus talaka yana nan cike da miki ko'ina a jikinsa. Watakila yana da wani cuta. Watakila wadansu ne sun yayyanka jikinsa saboda mugunta. Watakila su mikin da suke a jikinsa saboda ba ya cin isashen abinci mai kyau kamr madara, da ganye, da nama ne.

6

Liyazarus ya yi marmamrin abinci. Da zai ji dadin burbudin abincin da suke faffadi daga teburin mai arzikin.



7

Karnuka masu yawa sukan lashe mikin jikin wannan talaka maroki. Suna sussuna kewaye da shi suna lashi mikin. Ya kasance babu wanda ya lura cewa Liyazarus yana mutuwan yunwa.



8


Wata rana da safe, Liyazarus bai farka ba. Wannan mayunwaci talaka, maroki marar aboki ya bar wannan rayuwa. Liyazarus ya mutu.
9


Farin ciki ya fara wa Liyazarus muddin ya mutu. Yesu ya ce mala’iku sun dauke shi zuwa wurin Ibrahim. Allah ya ta’azantar da Liyazarus.
10


Mai arzikin shi ma ya mutu. Duka kudinsa ba su iya cece ransa ba.
11


An binne mutumin. Watakila babban jana’iza ne. Watakila mutane sun yabe wannan mai arzikin saboda wayonsa da nasararsa. Amma yabon da suka yi masa ba su taimake shi ba. Mai arzikin nan yana wutan jahanama.
12


A cikin wutan jahanama, mai arzikin ya yi kuka, “Baba Ibrahim, ka aike Liyazarus domin ya soma dan yatsansa a ruwa domin ya saka a harshena; gama ina shan azaba a wannan harshen wuta.”
13


“A rayuwa ka kasance da kome da kome sai Liyazarus babu kome.” Ibrahim ya tunashe mai arzikin. “Yanzu Liyazarus yana hutawa kai kuma kana cikin azaba. Babu wani wanda zai iya ketare wannan ramin da ke tsakaninmu da kai.”
14

“Ka aiki Liyazarus ya ja wa ‘yan’uana biyar kunne.” Mai arzikin ya roka. “Ba na so su karasa a wannan wurin mai tsanani.”



15

“‘Yan’uwanka suna da Kalmar Allah,” Ibrahim ya amsa. Idan ‘yan’uwanka guda biyar din nan ba za su ba da gaskiya ga Maganar Allah ba a Littafi Mai Tsarki, ba za su ba da gaskiya ba ko da Liyazarus ya koma daga mattatu.



16

Sa’ad da Yesu ya gama labarin mai arziki da Liyazarus, watakila shugabannan addini sun tambaye kansu, “Ko ina kaunar arziki fiye da yadda nake kaunar Allah?” Yanzu sun san abin da zai faru idan ba su yi biyayya ga Kalmar Allah ba.



17

**Mai Arziki, Marar Arziki**

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Luka 16**

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

18

# KARSHE

44

60

19

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah: Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**

20